# *Aiyukan Raya Kasa*

| | | |
|---|---|---|
| KUADE | | |
| **Cibiyoyi Casa'in Afrika Zasu Sami Taimakon Dala Miliyan 14.** | **1min. 49secs** | **3** |
| *Kungiyoyi masu zaman kansu da dama zasu cigaba da aiyukan su Godiya ga Gidauniyar Ford.* | | |
| **Karin Maganar Raya Kasa** | **30secs** | **12** |
| *Manyan Afrika sun danno.* | | |
| HARKOKIN MULKI | | |
| **Ra'ayoyin Jama'a 'Yan Najeriya Basu Amince Da Shari'a Ba.** | **3min 18secs** | **6** |
| *Ra'ayin jama'a na farko a Najeriya kan shari'a da dama basu amince ba.* | | |
| KIWON LAFIYA | | |
| **Duniyar Da Ba Cutar Shan-inna.** | **4mins 31secs** | **8** |
| *Wata mace a Indiya ta baiyana irin abinda ta sani game da allurar rigakafin cutar shan-inna.* | | |
| **Kungiyar Kasa Da Kasa Zata Magance Zazzabin Cizon Sauro A Yankin Neja Delta** | **1min. 17secs** | **5** |
| *Kungiyar agaji ta Sans Frontiere zata magance cutar dake kisa a Nija Delta.* | | |
| BINCIKE | | |
| **Majalisar Dinkin Duniy Ta Bukaci Kasashe Masu Tasowa Suyi Nazari Kan Abinci Mai Rike Ciki** | **1min. 51secs** | **3** |
| *Kungi Abinci ta duniya (FAO) na karfafawa kasashen Afrika gwiwa da su shiga sahun duniya kan abinci.* | | |
| MATA | | |
| **Yarinyar Da Mafarkin Ta Ya Zama Gaskiya.** | **3mins. 45secs** | **45** |
| *Sara ta cimma burin ta duk da rasa kafar ta guda da tayi a hatsarin mota.* | | |
| **Unesco Ta Bukaci Mata Su Kafa Bajimta Banar 8 Ga Watan Maris** | **1min 37secs** | **4** |
| *Shirin da akayi na duniya kan bajimtar mata.* | | |
| **Matar Kasar Rwanda Na Rabon Maza Tsakanin Su Domin Samun Iyali.** | **3 mins 20secs** | **7** |
| *Kisan kare dangi ya sanya mata a Rwanda raba maza tsakanin su.* | | |

# *Yanayin Muhalli*

| | | |
|---|---|---|
| AIKIN GONA | | |
| **Birrai Abokanen Manoma.** | **1min 16secs** | **4** |
| *A kyauta manyan Birrai zasu sanya manoman koko yin arziki.* | | |
| **Taran Gajimare Ya Kano Sauki Ga Kauyen Dake Fama Da Fari.** | **2min . 56secs** | **6** |
| *Wani kauye ya samo dabara samun ruwa daga gajimare domin biyan bukatar ruwa.* | | |
| **Kajin Swaziland Na Fuskantar Karewa.** | **1min. 19secs** | **4** |
| *Kaji 'yan kasa a Swaziland zasu kare a duniya saboda rashin tasarin kula da dabbobi na gari.* | | |
| HAMADA | | |
| **Hanyoyin Al'ada Na Taimakawa Domin Kare Hamada.** | **4 mins 22secs** | **9** |
| *Hikima irin ta al'ada zata taimaka wajen kare hamada a Afrika.* | | |

BALA'I

| | | |
|---|---|---|
| **Bankin Duniya Na Taimakawa Kasashe Matalauta Domin Kare Bala'o'i.** | **58. secs** | **3** |
| *Hadin gwiwar kasa da kasa na taimakawa wajen rage asarar rayuka da dukiya kan bala'o'i.* | | |

GANDUN DAZUZZUKA

| | | |
|---|---|---|
| **Da Mun Sare Iyace Yanzu Nuna Kulawa Gandun Dazuka.** | **3mins. 58secs** | **10** |
| *Al'umar da ada ta dogara kan saran itatuwa, yazu ita ke kare gandum dani.* | | |
| **Hukumar 'Yan Gudun Hijira Ta Duniya Ta Himmatu Kan Kare Muhalli.** | **1min. 16 secs** | **9** |
| *An fara aikin tsabtace yankunan al'umar da ta karbi 'yan gudun hijira a sashin Arewacin Uganda.* | | |
| **Sabuwar Mnufar Gandun Dazuka Dake Tafe.** | **3mins. 7 sec** | **8** |
| *Sabuwar manufa kan dazuka na majalisar dinkin duniya ta kammala.* | | |

## *Sashin Yara*

| | | |
|---|---|---|
| **Labarin Al'umar Afrika Ta Tsakiya Kan Alfacari.** | **4mins. 49secs** | **10** |
| *Yadda Alfadari ya sami zanen sa baki-da-fari.* | | |
| **Yadda Pokapin Ke Kare 'Ya'yanta** | **5 mins 43secs** | **12** |
| *Yadda pokapin ke kokarin fidda "ya'yan ta daga hatsari.* | | |
| **Hawainiya Na Kashe Kanta Ne Domin Haihuwa?** | **2 mins 11secs** | **11** |
| *Mutane na kashe Hawainiya ne saboda bahaguwar fahimtar da sukayi mata.* | | |
| **Meyasa Kudaje Da Kekkesai Ke Rayuwa Gashi Basa Tsinanawa Mutane Komai?** | **58secs** | **12** |
| *Kudaje da kekkesai suna da amfani ga jama'a fiye da yadda ake zato.* | | |

# *Lamarai*

**Kungiyoyi Casa'in Na Afrika Zasu Raba Dla Miliyan 14 1min 49secs**

Kusan kungiyoyi masu zaman kasu casa'in na Afrika (NGO) zasu sami taimakon dala miliyan 14 daga Gidauniyar Ford a watani shida na farkon shekarar bara. Dukkan kudin taimakon suna daga ciking shirin Gidauniyar na kula da bangarori uku,wandanda suka hada da aiyukan raya kasa,dana zaman lafiya da adalci,dakuma harkokin ilmi dana addini.

An samar da taimakon ne tsakanin daya ga watan Fabrairu zuwa 31 ga watan Mayun 1999,wadanda suka kama daga dalar dubu dari uku zuwa dala miliyan daya kana aka badasu cikin watani uku zuwa shekara uku. Cibiyoyin da suka ci moriyar shirin sun fito ne daga kasashe 14 daga dukkan nahiyoyi hudu na Afrika. Kasashen kuwa sun hada da Masar,da Ghana da Kenya da Mozambique,da Namibia,da Najeriya,da Senegal da Saliyo,da Afrika ta Kudu,da Tanzaniya,da Tunisiya,da Uganda da Zambia dakuma Zimbabwe.

Daga cikin wadanda suka ci moriyar sun hada da cibiyoyin bincike,da Jami'o'i da aiyukan kare muhalli,da kula da shara dakuma shirukan taimakawa juna,da harkokin magunguna da wasan kwaikwayo,da kungiyoyin dake yaki da cutar kanjamau dakiwon lafiya da kauda bambanci tsakanin maza da mata da kare hakkin dan adam da tsarin demokuradiya da kare yara da sauran aiyukan kare da sauran aiyukan kare tursasawa jama'a.

Haka kuma akwai kare 'yan tsiraru, da tattalin arziki dana al'adu da sake ginakasa tare da ilmi kan harkokin na'urar internet.

An zabi wuraren da za a taimakwan ne danufin karfafa Gideuniyar ta Ford kan karfafawa jama'a gwiwa wajen dogaro da kai na cibiyoyin duniya tare da karfafashirin rage talauci da yin adalci da hadin kan duniya tare da cimma manufa.

*Ford Foundation Report*

**Bankin Duniya Na Tanimakawa Kasashe Matalaita**
**Dp Om Lare Bala'i 58secs**

Bankin duniya da hadin kan Gwamnatoci sun kaddamar da shirin taimakawa kasashe masu tasowa danufin kare bala'o' in dake faruwa daga Allah. Membobin kungiyar da aka kira hadin gwiwar duniya sun hada da cibiyoyi da jami'o'i da sauran kungiyoyi masu zaman kansu.

Kamar yadda Bankin duniya ya nuna bala'o'i na kashe mutane sama da dubu hamsin tare da lalata dukiya ta sama da dala biliyan 65 a shekarar 1998 kadai. Kusan dukkan mace-macen a kasashe masu tasowa ne inda mutane mafi talauci suke zaune.

Shidai wannan hadin gwiwa yayi nufin samawa kasashe masu tasowa ne kayan da zasu iya kare kansu a duk lokacin da irin wannan bala'in ya auku,irin su girgizar kasa da ambaliyar ruwa da mahaukaciyar guguwa,domin rage yawan asarar rayuka da ta dukiya da sukeyi.

***Addis Tribune***

**Majalisar Dinkin Duniya Ta Roki Kasashe Masu Tasowa Suyi 1min 51secs**
**Nazari Kan Abinci.**

Hukumar abinci ta duniya (FAO) ta bukaci cibiyoyin bincike a kasashe masu tasowa da suyi nazarin hanyoyi daban-daban kan kayan abinci dangin hatsi domin su sami sukunin takara da sauran kasashen duniya. 'Hanyar samun karin labarai kan abinci dangin hatsi zai taimakawa jama'a a kasashe masu tasowa su saida kayan su tare da takara a kasuwanin duniya,' Inji Morton Satin baban jami'in hukumar abinci ta duniya.

Ana samun staci cikin abinci irin su alkama,da dawa da shimakafa da dankali. Daga cikin kayan da ake amfani dasu da sitaci sun hada a biredi,da sinak da miyar taushe,da kaji,da kayan kamshi,da fauda,da madara. Haka kuma ana yin kaya irin su takardu da masana'atun yin tufafi da kayan agwaja irin na mata da masana'antun magunguna da na sarrafa karafa.

A yanzu haka akasarin binciken da ake yi na sitaci anayi ne a kasashen da suka cigaba,hakan tilas a canja muddin ana bukatar gina ingantaciyar kasuwar sitaci ta duniya daga kasashe masu tasowa inji Satin.

Hukumar FAO ta fara nazarin aiyukan kayan sitaci ne shekara daya da ta shige yanzu tana aiki tare da cibiyoyin bincike na Italiya da Thailand kan batun. Man gaba hukumar zata marawa aiyukan nazahiri,wadanda suka shafi sitacin.

Satin yace sitaci kamar sauran abubuwan da ake samu bai samu cin moriya ba daga binciken da ake bukata domin tabbatar da harkokin kasuwanci yadda ya kamata a duniya kabi daya.
*FAO*

**Birrai Abokan Manoma Ne. 1min 16secs.**
Biri abune dake da ban haushi a duk lokacin da ya shiga gonar ayabar ka,amma binciken da aka yi kwanan nan,ya nuna suna iya kara samun manoman Coaco ta hanyar cin wadanda basu nuna ba.

Binciken wanda ya ta'allake kan jajayen birran ne dake tsibirin Zamzibar a kasar Tanzaniya,Kirsten siex da Thomas Stuhsaker na Jami'ar Duke dakedurham a Arewacin Carolina ne suka gudanar,. Sun gano birran suna zaben Coacon ne kamar yadda mazauna tsibirin keyi suma.

"Tunda yake sunfi son wadanda basu nuna ba,lallai suna aiki ne kamar ma'aikatan da ba abiyan su,ta hanyar kara yawan coaco akan itacen da suke cin kamar yadda siex da Struhsaker suka fadi.

Sun gano daga itace Coaco shida wadanda basu nuna ba da birran suka ci bayan wata guda sai guda goma sha-3 suka tsiro. Haka kuma itacen da suka cire goma wandada basu nuna ba sai ga 17 sun fito,wannan kuwa wata sanara ce inji su.

Manoman kamata yayi suyiwa Birran godiya bawai kashe su inji jami'an.
*The Economist*

**Kajin Swazi Na Fuskantar Karewa 1min 19secs**
Wasu nau'in kajin kasar Saziland biyu na daf da karewa a duniya. Kajin sune da wadanda basu da gashi a wuya da masu kananan kafafu,wadanda yanzu basu da yawa. Jami'an Gwamnati sunce wata kila ancinye su ta wajen yin miya.

Ministan gona da jam'iyun gama kai na kasar Roy fanourakis ya dora laifin karewa kajin kan rashin bullo da dabarun zamani na kiwon kaji,da rashin kula da dabobi dakuma rashin tsari na gari.

A halin yanzu dai wasu kungiyoyi uku na duniya,hukumar raya kasa UNDP,da hukumar abinci (FAO) da kungiyar raya kasashen kudancin Afrika (SADC) sun kaddamar da shirin inganta noma da kiwon dabbobi ta yadda za a magance rashin tabuka abu kan kiwon dabbobi a Swaziland.

Fanourakis yayi fata da wannan matakin,'ina mai imani kan wannan tsari da muka kaddamar zai taimaka wajen inganta harkokin noma da jama'ar mu inji shi.
*PANA.*

**Unesco Ta Bukaci Mata Suyi Bajimta Ranar 8 Ga Watan Maris. 1min. 37secs**
An roki daukacin dafofin yada labarai da su baiwa mata 'yan jarida damar samun gindin zama a jaridar su da labaran su a ranar mata 'yan jarida ta duniya watau 8 ga watan Maris.

Koichiro Matsuura,babban darektan hukumar UNESCO saida yayi roko tun farkon watan Fabrairu kan dukkan kafofin yada labarai da su baiwa wannan rana 8 ga watan Maris muhimmanci ta hanyar ganin matan sunyi bajimta.

'In 'yan jarida da sauran kafofin yada labarai da suke wakilta sun basu damar haduwa da juna domin samun nasarar shirin,zai zo daidai da tsarin jami'an tace labaru inji ta.

Ta wannan hanyar bada dama ga kowa ne UNESCO take son jaddada samun labarai ba tseko ta hanyar baiwa kowa dama daidai-wa-daida ta yadda zamu zama manyan jami'an tace labarai batare da nuna bambanci maza da mata ba ko jinsi ko addini.

La'akari da wasu kafofin yada labarai wadanda tuni mata ke shugabancin su kungiyar ta UNESCO ta kyale su da su yanke shawara kan yadda yafi dacewa su kallamar da shirin.
*UNESCO.*

**Wata Kungiya Ta Duniya Zata Magance Zazzabin Cizon Sauro A Yankin Neja Delta.** **1min. 17secs**

Bayan ziyara sau biyu domin tantance matsayin kiwon lafiya a yankin Neja Delta yankin da akafi rigima ciki a Najeriya,wata kungiyar da tayi fice a duniya kan aiyukan jinkai Sans Frontiere (MSF) ta yanke shawarar gudanar da shirin yaki da zazzabin cizon sauro acan.

Kungiyar daga binciken da ta gudanar ta gano cutar itace ta daya wajen kisa wanda ta kashe kimanin mutane 100,000 a yankin mai arzikin manfetur.

Aikin zaiyi sansani a Yenagoa hedkwatar jihar Bayelsa,tare da ma'aikata na farko kwararu biyar da sauran jami'ai 'yan Najeriya su 30. za akuma bullo da shirin tafi da gidan ka domin tabbatar da ganin aikin yakai ga daukacin jama'ar na yankin Neja Delta.

Baya ga zazzabi da zazzabin cizon sauro,za a kuma kafa tsarin rigakafi dana wayar da kan jama'a.

Ita dai kungiyar ta Medicine sans Frontiere tana Najeriya tun 1996 bayan da cutar sankarau ta barke a arewacin Najeriya kana daga bisani kungiyar ta bada taimako kan wasu manyan cutuka daga bisani. irin su lolera da sankarau da ciwon shawara.
*Medecines Sans Frontiere.*

**Hukumar Kula Da 'Yan Gudun Hijira Ta Tsaya Kan Kula Da Tsabta** **1min. 16secs**

Hukumar kula da 'yan gudun hijira ta duniya ta dukufa kan yekuwar tsabtace sansanonin 'yan gudun hijira a sashin arewacin Uganda.

Da yake magana kwanan nan a taron karawa juna sani a Kampala ta Uganda Adera Tsegaye mukaddashin wakilin hukumar,yace hukumar ta sami dala miliyan 42 daga ma'aikatar tsimi da jam'iyun gama kai na Jamus (BMZ) domin kyautata yanayin muhalli tare da rage irin abinda ke akwai ga jama'ar da ke karbar bakwancin su 'yan gudun hijira dake arewacin Uganda. Za a kula da matakan dake akwai ciki har da dazuka,samar da kayan aiki da ruwan sha da shirin kula da muhalli ga 'yan gudun hijira da jama'ar dake tare dasu. inji Tsegaye.

Wanna sabon shirin bashi ne na farko ba a yankin. An gudanar da irin wannan a arewacin na Uganda tun daga 1996 zuwa 1999. Tsegaye.

Wannan sabon shirin bashi ne na farko ba a yankin. An gudanar da irin wannan a arewacin na Uganda tun daga 1996 zuwa 1999. Tsegaye yace sabon aikin,za afadada shi domin taimakawa karin kula da muhalli a unguwanin da 'yan gudun hijirar kamar su Koboko,da ajumani dakuma Moyo,wadanda suke da dazuzzuka.
*New Vision:*

**Sarrafa Giza? Gizaiya Kawo Sauki Ga Kauyen**
**Dake Fama Da Fari** **2mins. 56secs**
Caleta Chungungo,wani kauye ne dake karkashin tsaunuka,dake fama da fari a kasar Chile dake kudancin Amurka,wanda ya sami hanyar sarrafa giza-gizai.

Caleta na bushewa tare da karewa, har yazuwa lokacin da masana yanayi na Chile masu bincike na Canada da sauran kungiyoyi na duniya suka tsaida shawarar yin amfani da abinda garing yafi tamaka dashi CHAMACHACA, watau gizagizan dake wuce ta garin kusan duk dare.

Kame giza-gizai wata dabara ce kamar sanya bakar gizo cikin kwalba. Amma mazauna kauyen Caleta sun gano hanyar yin hakan. Sun iya yadda sukeyi domin matso ruwa daga gizza-gizan dake bushe ta hanyar yin amfani da raga. Suna da raga 86, wadanda akayi daga nailon, wadanda aka rue tare da barin ramuka a inda akayi tanadin tara ruwa, wanda girman sa yayi kamar allon da ake kafawa domin talla akan tsaunin dutse domin tara ruwan wucewa.

Ruwan dake fadowa daga giza-gizan su ake tarawa, wanda kuma suka tanadar da fili mai fadi domin wannnan, in har sun girma sai su rika fadowa ta wadan nan hufin ragar zuwa inda suke taruwa daga nan sai tacewa. A ranar da tayi kyau ana iya samun lita 700 ruwa.

Bakamar sauran makwabtan sa ba kauyen Caleta na samun sauki daga kogunan dake kusa. Babban abin ma kauyen na nan ne kan hanyar da babu ruwa sam, inda ba a wuce samun 7oomm a shekara. A sakamakon haka Caleta mai mutane 350 tilas sai sun dogara kan motocin dake kawo musu ruwa daga wasu wurare domin rayuwar su. Hakan na da tsada aikun musamman kauyawan dake hannu baka hannu kwarya.

Amma daga wannan tsari na amfani da giza-gizai suna samun ruwa lita 300,000 a kowani wata kimanin kowani mutum na samun lita 30, kuma abinda suke kashwa bai fi kashi uku cikin biyar na abinda suke sayen ruwa ba.

Wannan hanya mai sauki da saukin samu na ruwa ya taimakawa manoman Caleta kamar yadda Benjamin Quijandria wani kwarare dan lLatin Amurka a hukumar kula da aikin gona dake Roma ya fadi. Man oman dake kauyukan dake kusa sun fara nuna sha’awa kan wannan aiki. Suna duba yiwuwar fadada aikin domin rage tsadar kudin nomena rani a gonakin su.
*The Economist.*

## *Rahotanni*

**Ra’ayin Jama’a Kan Shari’a** **3min 8secs**
Ra’ayin jama’a da aka gudanar kwanan nan, da kamfan in RMS yayi, ya nuna wasu ‘yan Najeriya basuyi maraba da bullo da tsarin sharia’a a da gwamnatin jihar Zamfara dake area maso yammacin Najeriya tayi ba cikin watan Nuwamba 1999. Amfani samun rashin amincewa bisa tsarin kabilanci dana yanki, kuma akasari daga mabiya addinin kirista dake kudancin kasar. Haka kuma wasu daga arewacin kasar ma sun aiyana rashin amincewar su cikin Musulmin da kiristoci. Amma duk bai isa ya hana bullo da tsarin shari’ar ba a wasu karin jihohin takwas ta hanyar samun rinjaye mafi kankanta daga jihohin.

Samfur daga mutane sama da 5,000 daga dukkan jihohin tarayya banda zamfara kamfanin RMS ya gano cewa kimani rabin su basu amince da bullo da tsarin ba a jihar Zamfara, yayinda daya bisa uku suka amince. Yawanci ‘yan kudancin kasar ne basu amince ba a jihar Lagos kusan kowa bai amince ba, sai gabashin kasar dakuma yammacin kasar. Ba agudanar da jin ra’ayin ba a Zamfara saboda tsaro.

Daya daga cikin mutane uku a arewacin Najeriya ne basu amince ba, yayinda daya cikin goma suka yi tsit da bakin su. Wannan kuwa yafi wadanda aka zata idan aka bi yadda Gwamnatocin Zamfara da Neja suka fadi na samun amincewa baki daya game da bullo da tsarin shari’ar. Koda shike rashin amincewa kan bullo da tsarin shari’a yayi yawa, duk da haka shirin ya sami goyon baya a jihohi akwai akasari daga sashin arewa

maso yamma. Duk da haka ra'ayin ya nuna jihar Neja an sami kashi 31 cikin dari na reshin amincewa jihar Kaduna kashi 58 cikin dari. Rashin amincewa a jihohin Bauchi da Adamawa da Gombe da Nasarawa, da Taraba da Pilato dakuma Kogi ya tashi ne tsakanin 34 zuwa 75 cikin dari.

Haka kuma ra'ayoyin jama'ar sun nuna biyu daga cikin kowani mutum uku daga arewaci da kuma daya daga ciki uku na musulmin arewa, suna ukatar gwamnatin tarayya ta duba wannan lamari game da hihar Zamfara, Shugaba Olusegun Obasenjo bai fito fili yaki ko ya aminced da maganar shari'ar ba.

'Wannan rashin tsaida shawara kan batun na baiwa sauan jihohi kwarin gwiwar cigaba da yin mahawa wajen bullo da tsarin shari'a kamar yadda binciken ya nuna.

Ikirarin da Gwamnan jihar Neja keyi na cewar yayi daidai bisa bukatar akasarin al'umar jihar yayi daidai. Haka kuma ya nuna hujjoji da ke nuna shari'a ba ra'ayin al'umar jihar Kaduna bane inda ake kokarin bullo da tsarin.

Haka kuma inciken ya nuna yadda kiristoci suka nuna rashin amincewar su game da ullo da shari'ar, ba kamar yadda wasu musulmin suka nuna amincewar su da bullo da tsarin shari'ar kiristanci in har akwai.
R M S.

**Matan Rwanda Na Raba Maza Domin Samun Iyali** **3mins 20secs**
Rashin samun miji Maatan kasar Rwanda wadanda suka rasa mazajen su da 'ya'yan su a sanadiyar kisan kare dangi da ya auku a shekarar 1994, yanzu sun fara raba maza tsakanin su danufin samun iyali. Hakan ya haifar da fargaba tsakanin ma'aikatan kiwon lafiya, wadanda suka ruwaito kan karuwar mutanen dake kamuwa da kwayoyin cutar kanjamau bisa wannan tsarin.

Josephine Nyananwandakusi, wanda ta rasa mijin ta da 'ya'yan ta hudu cikin biyar a lokacin kisan kare dangin, ta matsa ainun wajen sake samo 'ya'yan da ta rasan.
Tace ashirye take ta fuskanci duk wani hatsari kan wannan.

Rayuwa a Rwanda batare da miji da 'ya'yan ba ba rayuwa bace, inji ta. Yanxu abune mawuyaci samun miji, amma akalla zan sami 'ya'ya inji ta.

Domin samun haka ashirye take domin raba maza da wasu matan irin ta. An kashe maza da dama, wasu kuma an saure su saboda hannun da suke dashi wajen kisan kuma babu tabbas na mata irin ta su sami miji. Amma ta hanyar raba mazaje Nyinawanakusi ta sanya kan ta cikin hatsarin kamuwa da kanjamau.
Nasan akwai cutar kanjamau, amma samun iyali shine mafi muhimmanci inji ta.

Shirin raba maza, wanda ake kira kwinjira yana yaduwa a yankunan karkara na kasar Rwanda tun lokacin kisan kare dangin. Yafi tsanani a tsakiyar kasar inda kisan ya auku ainun. Ance kimanin mutane 800,000 ne suka mutu a kisan na shekarar 1994. A wasu gundumomin kam mazajen da suka rage basu fi kashi 20 cikin dari bane na yawan jama'ar.

Tuuni Rwanda na fuskantar hatsari cutar kanjamau. Kimanin kashi 11 cikin dari na jama'ar kasar ne aka kiyasta sun kamu da kwayoyin cutar HIV, tuni jami'an kiwon lafiya sun radawa cutar kanjamau sunan sabuwar kisan kare dangi. Dr. Ildephonse kamali,wanda ke aiki a Asibitin kabgayi a wajen garin Gitarama yace kashi hamsin cikin dari na wadanda aka gwada duk suna da mutar ta kanjamau.

Darektan shirin kula da kare yaduwar cutar Innocent Ntaganira yace masu fama da cutar kanjamau ke kwance a kashi 60 cikin dari na gadajen Asibitin,kana fiye da mutanen Rwanda dubu metan,dubu hamsin yara duk sun mutu a sakamakon ita wannan mugunyar cutar.

Rokon jama'ar da suka ketare rijiya da baya wajen kisan kare dangi mafi muni tun yakin duniya na biyu na da wuya inji Ntanganira. Wadanda suka ketare rijiyar sunce fargamar me zasuyi kuma,tunda shike cutar bata kisa sai bayan shekaru goma. Matan sunce in har kanjami hatsari ne da zasu fuskanta ashirye suke domin sake samun iyali.
*Deseretnews.*

**Za'a Bullo Da Sabuwar Manufa Kan Dazuzzuka Ta Duniya. 3mins. 7secs**
Masu kare dazuzzuka dakuma dangantakar su da tattalin arziki na daukar muhimman matsayi game da bullo da sabuwar manufa a Amurka dakuma hukumar hare gandun dazuka ta majalisar dinkin duniya (UNDP).

Babban taron kasa da kasa kan harkokin gandun dazuka na majalisar dinkin duniya a New YOrk daga 31 ga watan janairu zuwa 11 ga watan Fabrairu,ya tattauna kan shirin da akayi na kulawa dakuma kare dukkan gandun dazukan da ake dasu a duniya kana a can Amurka maganar dazuka ta sami shiga cikin kasafin kudin shugaba Bill Clinto na 2001,wanda akayiwa taken 'duniya mai launin tsanwa',wanda za a tafiyar ta hanyar yafewa kasashe masu talauci bashin dake kan su muddin suka amince wajen kashe adadin kudin da ake bin su ta hanyar kula da dazuka.

Wanna babban taron na Gwamnatoci kan gandun zasukan shine na hudu kuma na karshe shawarwarin da ya bayar na karshe za a gabatar gaban hukumar kula da raya kasa ta majalisar dinkin duniya.

Taron ya kuma tattauna kan tsari da dokoki game da kare dukkan dazukan da ake dasu. Haka kuma yayi nazari kan dalilai dake janyo gurbacewar dazuka,dakula da kare dazuka da irin bukatun dasashe da basa iya kare dazukan su yadda yakamata dakuma dazukan dake da ruwa,da matsalar wutar daji da musaya kan fasahar dazuka tare da samar da kudaden da za a tafiyar da aiyuka.

Ana samun gushewar dazuka a kasashe masu tasowa saboda dalilan samar da katako dakuma samun filayen noma da sauran su inji rahoton hukumar UNEP. Yanayin duniya a shekara ta 2000'Anyi asarar kadada miliyan 65 na dazuzuka tsakanin 1990 zuwa 1995 daga cikin adadin kadada miliyan 3,500 na dazuka dake akwai. Kana inganci ragowar dazukan na fuskantar barazana daga matsi daga wutar daji ambaliyar ruwa dakuma sauran aiyuka.

Babban darektan hukumar UNEP Mr. Klaus Toepfer ya gabatar da kasida a wajen taron wanda ke bukatar mahalarta taron da suyi nazari kan alherin dake akwai da asuka kama daga na tattalin arziki,da masana'an tu da al'adu dakuma zamantakewa da sauran aiyuka.

'Kula da gandun dazuka da kare yanayin muhallin mu abune dake tafe tare bisa kokari cimma daidaito kan cigaban tattalin arziki....tilas mi dakile abubuwan dke janyo talauci,da kamfar ruwa da tauyewar makamashi dakuma tauyewar dazuka'.

Mr. Toepfer yace za afara aiki da manufofin hukumar ta UNEP game da manufar nan ta aiwatarwa,tare da bada himma wajen kara inganta tsarin hadin kai na kasa da kasa da kungiyoyi tare kuma da yarjeniyoyi.
*UNEP*

**Duniyar Da Ba Cutar Shan-inna: 4mins. 31secs.**
(Yayinda duniya ta maida hankali kan Afrika da Asia domin kauda cutar shan-inna wata 'yar jarida a India ta gurgunce bayan da akayi mata allurar rigakafi,amma tace allurar itace mafi dacewa domin kauda cutar).

Rana ta shida cikin mako a watan Oktoba 1967,na sanya kaya na dakuma takalma ina tare da kakana,domin karbar allurar rigakafin cutar shan-inna,ina tafiya ina wasani domin zuwa gun allurar,ban sani ba ashe wannan shine na karshe da zanyi tafiya bisa kafafuwa na biyu.

Bayan da muka dawo,sai na fara jin ciwo a kafafu na,nan da nan sai zazzabi ya rufe ni. Ba zan taba mantawa da wannan daren ba a rayuwa ta. Kakana sai ya dauke ni zuwa bayan gida,kafata ta hagu bata tsayawa ga kuma dan karen zafi.

'Yan kwanaki da suka biyo baya yara iri na sai zuwa sukeyi Asibiti a Jaipur fadar jihar Rajasthan dake yammacin kasar India. Bayan mako biyu ne da aka auna sai aka gane ashe cutar shan-inna ne ta bulla. Sauran wata uku nayi bukin cika shekara uku da haihuwa,gashi na zama gurguwa har abada,a shekarar 1967. Bullar annobar cutar da ta game kasashe masu arzikin masana'a tu na kusan shekaru ashirin daga1940s zuwa 1960s ya gurgunta dubban yara kowace shekara,saida aka sami ingantacen maganin rigakafin sa tukuna.

Dr. Jonas Salk na Amurka shi ya bullo allurar rigakafi marasa inganci IPV a shekarar 1955,makashi ne cutar shan-inna tilas ayi mata rigakafi. abokin mahaiyar Dr. Salk,watau Dr. Albert Sabin,ya kirkiro da sabuwar allurar da ake digawa a baki OPV,wanda ya kunshi mataki biyar.

A Indiya ana shigo da allurar ta OPV ne daga kasar Rasha,saidai ana bukatar wurin anada mai sanyi domin kada maganin ya lalace,wanda babu shi a wancan locaci a Indiya. Kuma yanzu an sami wata na'ura dake auma ko maganin ya hadu da zafi (VVM).

wasu sunyi ikirarin cewar,allurar da akayi min tare da sauran yara dake fama da irina ta kare aiki ne. Wasu kuma sunce an bar allurar ne a filin jirgin sama har rana ta buga,wanda bai iya komai.

A shekarun 1960 babu wayewar kai game da allurar rigakafin cutar shan-inna a India babu wani matakin da aka dauka,domin haka rayuwa ta gurgunce ga yara iri na. Mahukuntan sun baiyana cewa wannan annoba ce kafin rigakafin.

Daya daga cikin allurai miliyan uku da akeyi na OPV ake danganta ta da gurguncewar allurar rigakafi. Saidai alfanun dake tattare da allurar rigakafin na dayawa wanda dubban daruruwan yara ke cin moriyar sa a kowace shekara. Hukumar lafiya ta duniya WHO ta fi bada muhimmanci ga allurar OPV,wajen kauda cutar ta shan-inna fiye da allurar ta IPV. Ana kuma tafiyar da shirin a kowace shekara a duniya.

Da nake rubuta wannan yanzu,shekaru 31 daga bisani,har yanzu babu maganin warkar da cutar shan-inna. Amma akwai rigakafin ta dakuma yekuwar da akeyi a duniya baki daya domin kauda cutar kafin karshen wannan shekara.

Yau cutar shan-inna wanda ake kira da cutar gurgunta mutum,an kauda tita a sassa dayawa na duniya. Wuraren da cutar ta saura sune yankin Saharar Afrika da kudancin nahiyar Asia.
*Neena Bhandari*

**Hanyoyin Al'adu Na Tatimakawa Wajen Kare Hamada 4mins. 22secs**
An gudanar da wani safiyo da nufin tara bayanai kan hanyoyin al'adu na kula da albarkatun kasa da manoma keyi dakuma wadanda ke zaune a bakin iyakar saharan Afrika. An tafiyar da safiyon ne danufin inganta harkokin samar da abinci,da rage talauci tare da karfafa harkokin kula da aiyukan bincike.

Wanda kungiyar kasa da kasa kan aikin gona da kula da hamada dakuma bincike ta gudanar,safiyon da aka hada ya kunshi hikima bisa al'ada,wanda ke kula da muhalli haka kuma an gano hikimar mazauna yankunan hamada tana bacewa cikin hanzari.

'Ka'idojin nan da tsarin dake taimakawa mazauna bakin yankunan hamada su zauna lafiya da sauran halittu,sai dade karya su akeyi,bawi da gangan ba sai saboda rashin wani zabi da za abi'kamar yadda safiyon yayi bayani. an kaddamar da shirin na mazuna bakin sahara ne domin kare hikimar dake akwai.

Al’umar Turkana dake arewa maso yammacin Kenya sukan hukunta duk wanda ya sare itace daga gandun dajin Moro Anyache,wanda sukayi imanin cewar can ne asalin su. Haka kuma al’umar suna kare dazukan dake da alaka da iskokin mutuwa,kana suna da dokoki na shekara da shekaru dake taimakawa tsirrai da itatuwa da ake samu a bakin kogi da gidaje. Magabata ke da dazuka,amma kare dazukan alhaki ne da ya rataye kan al’uma.

Haka kuma Burkina Faso wasu mazauna hamada suna dasa itatuwa irin su acacia a bakin gonakin su,saboda la’akarin da sukayi na cewa irin wadan nan itacen suna taimakawa wajen kara yawan kayan amfanin gona. Haka kuma suna karfafa rike amfanin gona. Haka kuma al’umomin basa yarda ayi amfanin da wasu nau’in itatuwa domin girki,domin ana cin ‘ia’uan su a lokacin rani,lokacin yunwa.

Kafin ‘yan shekarun nan da makiyaya suna kiwon dabbobin su a sashin arewa ne da damina,kana su komo kudu da rani domin samun abincin dabbobin su. Ana shuke-shuken kayan gona,kana a barfilaye domin inganta dausayi. Amma yanzu da jama’a sukayi yawa ba abin wannan al’ada saboda karancin gonaki.

Yayinda maganar anayi mata lakani da fada tsakanin masu aikin yi da masu kula da muhalli,Jungwirth,wanda ta fito daga iyayen dake sana’ar katako,tayi imanin cewar akwai hanyoyin da suka dace wajen kula da dazuka,wanda kuma zai inganta tattalin arzikin kananan garuruwan. ‘yan raji kare dazuka dake cikin amurka sunyi ta gwada hanyoyi domin horas da wadanda suka daina aikin katako,domin samun sabuwar sana’a daufin kare albarkatun dajin,wanda kuma kwalliya ta biya kudin sabulu.

Wannan aikin daga bangaren ainihin babban aikin da ake kira kare dazuka daga al’uma’wanda ke shigar da mazauna karkara danufin kula da dazukan. Kauyukan dake samar da katako irin su Hayfork dake kokarin rayuwa,ya zama zakaran gwajin dafi.

A shekarar 1993 Jungwith ta fara gudanar da bincike a cibiyar horaswa bisa wannan sabon tsarin kula da dazuka domin garin su. a shekarar 1996 a sakamakon aikin ta a Hayfork,an gaiyace ta da shiga cikin hukumar nan ta majalisar dokokin Amurka mai kula da gandun dazuka,wanda kuma ke samun taimako daga gidauniyar Ford.

‘Sunadaukar kwamiti kan bincike,daya kan manufa daya kan ilmi’inji Jungwirth. ‘Nace yaya maganar kwamiti kan al’umomi kuma? domin koda wace iri manufa kuka yi ko kuka gano a binciken ku ko shirin ilmin ku in babu sami goyon bayan al’uma ba ab za asami nasara ba.

Yau kwamitin al’uma,wanda take shugabanci ya game kasa baki daya,yana da kungiyoyi 300 kuma shine jigon aiki kan gandun dazuka a Amurka.

Jami’an gandun daji daga nesa kamar India,Mozambique da China sun zo Hay fork domin koyon aiyukan cibiyoyi tare da karawa juna sani. Sauran aiyuka da shawarwarin kwamitin yanzu haka kauyuka da garuruwa suna gwadawa.

Jungwirth ta lura da cewar aiyukan al’uma tilas ne su hadu da sauran aiyuka,domin haka gari irin Hayfork na iya kirkiro sassa da dama na tattalin arziki,domin rayuwa. A kusan kowace rana tana kaffa-kaffa. Saidai akwai aiki ja a gaban ta.

*Ford Foundation.*

## *Sashin Yara*

**Tatsuniyar Mutanen Afrika Ta Tsakiya Kan Alfadarin Farko 4mins. 49secs**

A farkon duniya,yayinda komai na sabo a doron kasa dabbobi duk iri guda ne babu wata dabbar dake da kaho ko launi ko wata siffa ta dabban. Amma a kusa da katon kogo dake kusa da katon tabki,akwai kahuna iri-iri manya da kanana dakuma launuka iri-iri.

Dukkan dabbobin dake zaune a filin dake da ciyawa,suna kiwo,sai aka kira su aka shaida musu cewar gobe da safe,sai kowace dabba ta shiga cikin kogon ta zabi irin kahon da take so dakuma launin da yafi dacewa da ita. Domin haka ko wace dabba tana Allah-Allah safiya tayi domin taje ta zabi kaho da launin da take sha'awa.

Kowace dabba na doki,banda alfadari,wanda babban abinda ya dame shi shine cikin sa. A gaskiya ma kowace dobba ta san halin alfadari da ci. Yayinda kowace dabba ta kama hanya zuwa kogo da sanyin safiya,alfadari bai tafi tare dasu ba. Yace in har zaiyi doguwan tafiya kamar haka,to kamata yayi ya cika cikin sa tukuna,baiga wani abin doki ba da sauran dabbobin keyi kan samun kaho da launi. Koda shike sauran sauran dabbobin sunce dashi yazo su tafi yace dau su cigaba gashi nan tafe,in ya karya kumallo. Ya fadi hakan ne kuwa yayida ya hambudi ciyawa. Sauran dabbobin sukayi tafiyar su suka bar alfadari.

Bayan sa'o'i da dama sai alfadari ya ga yayi tatil da ciyawa,daga nan sai ya kama hanya zuwa kogo yana bin burtalin da sauran dabbobin suka bi. Yayinda alfadari ya kusa da kogi sai yaga wasu daga cikin dabbobin suna dawowa tuni har sun zabi kaho da launin da suke da sha'awa. Giwa ta zabi launin toka kana ta hada haure guda biyu. Zaki ya zabi launin dabbare-dabbare mai digon baki.

Daya bayan daya,alfadari na kallon su,suna wucewa da sabbin launi da kahon da suka zaba. Daga karshe yana dab da shiga kogon,sai alfadari yaga karkanda. Karkanda tafi gani kurkusa,ta zabi launi masu girma daban-mai makon ta sanya kahon a kan ta kamar sauran dabbobi,sai karkanda ta dora kahon kan hancin ta.

Yayinda alfadari ya shiga cikin kogo sai ya tarar ba abinda ya rage sai launin fari da baki buga da kari kahuna sun kare. Bayan doguwar tafiya gashi kuma ya fara jin yunwa,domin haka sai yayi sauri ya dauki fari-da-bakin da ya rage ya sanya kuma ya karbe shi amma shi bai damu ba,kuma bai damu da rashin kahon da yayi ba. Bayan kowace dabba ta koma ne sai sukeyiwa juna murna bisa irin zaben launi da kahunan da sukayi. Yayinda alfadari ya komo bai damu da kowa ba sai ya cigaba da cin ciyawa abin sa. Sauran dabbobin da suka ga irin abinda alfadari ya samu na fari da baki,sai suka shiga yi masa ysiya da dariya.

'Dubu sarkin hadama alfadari cikin sabon launin da ya samu,kuma bai da kaho'inji sauran dabbobin,daga bisa sauran dabbobin kuma suka shiga rera masa waka suna yi masa shegan taka.

Shidai alfadari bai damu ba. Ba Kaho bane abun da muwa,abin damuwa shine ka samu abinci mai yawa ka cika ciki,inji alfadari. Shine hae yanzu alfadari baida kaho amma zaka ganshi a koshe bul-bul-bul,da zanen sa fari da baki.

*When Hippo Was Hairy:*

**Hawainiya Na Haihuwa Ta Hanyar Kashe Kanta? 2mins. 11secs**

Akwai labaran al'ajabi a gabashin Afrika na cewar kafin hawainiya ta hailhu sai ta hau kan itace ta fado cikin ta ya fashe 'ya'yan su fito. Koda yake wannan babu gaskiya a ciki, amma dai shike yaduwa. Me yasa wannan al'ajabin ya samo asali? wata kila wata rana wani ya ga hawainiya ta hau itace ta fado cikin ta ya fashe 'ya'yan ta suka tito.

Yaya hawainiya ke haihuwa? wasu nau'in hawainiyar suna haihuwa ne kan bishiya su bar 'ya'yan can. Yayinda wasu nau'in kuma ke saka kwai a kasa, dumin kasa ke taimakawa wajen kyankyasar kwan.

Mutane da dama suna tsoron hawainiya, don haka suke kashe ta. Wannan kuwa saboda watakila canja launi da takeyi. Hawainiya tana iyacanja duk launin da take so tana kuma sarrafa idanun ta ta kalli duk kusurwar da take so a lokaci guda. Dukkan wannan abu na tsoratar da wasu mutane. Amma sukan taimaka wajen kare su tare da sama musu kwarin da take ci.

Hawainiya tana canjawa zuwa launuka daban-daban. Daga launin kore zuwa algashi da rawaya da baki. Tana iya maida launin sitin ko farfara, tana iya kuma kara dabbare-dabbare domin fiddo ta sarari. Saboda tana yin irin wannnan ne wasu mutanen dauka tana da dafi.

Amma batada shi. Hawainiya bata da hatsari ga mutum. Bakamar yadda wasu ke zato ba mutum ba zai mutu ba ko canje launin sa in hawainiya ta cije ka. Hawainiya tana taimakon mu ma ta wajen cin kwari dake yi mana ta'adi a gonaki. Saboda haka ne ma ya kamada mu kyale su su cigaba da rayuwa.
*Chongololo*.

**Meyasa Kyankeso Ke Rayuma Tunda Basa Taimakawa Mutum? 58secs**
Wannan wata kykkyawar tambay ce, kuma amsar ta na da alaka kan kowace halitta tana da rawar da zata taka. Kyankyasai da kudaje suna daga cikin halitun da Allah Yayi dake nasaba da kazanta. Suna cin matatun dabbobi kuma kuda na daukar ruwan furanni daga wannnan zuwa wancan.

Kwari da dama ne ke tare da dan adam. Kudaje da kyankyasai suna samun abincin su ta najasar da adam, da sauran datti. Abin taka ici wani sa'ilin sukan dauki guba su saka cikin abincin mu. Hakan yakan sanya mu ciwo, domin haka kamata yayi mu rika rue abincin mu, kana mu rika tsatace ciki da wajen gidajen mu. In munyi haka za mu rage yawan kudaje da kyankyasai dake damun mu.
*Chogololo*

**Karin Maganar Raya Kasa: 30secs**
Kudancin Afrika na da albarkatu da dama, kama da ma'adinai da makamashi fiye da gabashin Asia, yayinda ita kuma take da albarkatun jama'a. Yanzu da yake Afrika ta kudu ke fage, mun fara magance raunin mu na albarkatun jama'a. Nayi imanin zuwa tsakiyar karni na 21 zamu bugi kirjin cewar Afrika ta kudu ta kawo karfi irin na gabashin Asia.
*Christon Tembo, Vice President of Zambia/The Courier*

**Yadda Pokapin Ke Kare 'Ya'yanta 5mins. 43secs**
Pakara ta cika son 'ya'yan ta, sai ta birkice. Sai ta fara sa ido domin ko akwai abinda zai nuna mata yadda 'ya'yan nata sukayi. Tana dubawa sai taga takun sawun muzurun dawa. Wannan tsinanen barawon inji palara. Sai na kama shi. Tayi ta bin sawun har zuwa wata katuwar bishiya. Inda ta tabbastar da cewa nan 'ya'yan ta suke domin taji kukan su.

Tana cikin wannnan hali sai wani tsoho yazo. Yaga irin halin da take ciki, sai ya tambaye ta abinda ya faru. Tace dashi 'ya'ya nane muzurun dawa ya ace ya buya dasu kan wannnan bishiyar.

Kada ki damu inji tsohon, zan karbo miki su. Sai ya fara saran bishiyar daga tushe har sai da ta fadi kasa. Paakara tayi sauri ta dauko 'ya'yan ta, yayinda muzurun dawa ya diro ya sheka a guje cikin daji, tsohon kuma ya bishi a guje.

Yayinda sukayi da gudu cikin sunkuru, sai kurege ya hade dasu, tsohon baiga hadewar su ba sai yayi ta bin su da gudu yana zaton muzurun dawa yake bi kadai. Abokin na ka faye gudu inji kurege, ya tambayi muzurun dawa me ya faru ne ma? Wannan tsohon ne ke bi na na saboda na sace 'ya'yan pakara inji muzurun dawa. Karkadamu inji kurege saboda kai aboki na ne zan taimake ka. Washegari kurege ya nemi pakara inda suka fara tai. Ya gai sheta Nhungu naji ance muzurun dawa ya sace miki 'ya'ya jiya. Abinda kike bukata shine wuri mai tsaro domin ajiye su. Kuma gashi ina da wuri mai kyau cikin rami na, inda zaki iya ajiye su batare da fargaba ba, in kina bukata.

Nagode sosai kurege, domin pakara tajidadin wannan taimako, sai ta kwashi 'ya'yan ta zuwa ramin kurege ta ajiye su,. Amma yayinda kurege da pakara suka bar ramin kowa ya kama gaban sa, sai taji kurege na shaidawa muzurun dawa zo da quri. Pakara ta zuba 'ya'yan ta a rami na. Ashe pakara na ji, ai ta ganed yaudara ne nan da nan takoma bakin rami inda 'ya'yan ta suke tayi likimo. Da muzurun dawa ya iso sai yaga pakara yace kurega ya yaudare shi ya kyale pakara da 'ya'yan ta.

Bisa fushin abinda kurege yayi mata sai pakara ta sami sarkin dawa zaki Khala. Ta kwashi labari ta gaya masa abinda ya faru tsakanin ta da kurege, kana ta nemi taimakon zaki domin koyawa kurege darsin da ba zai manta ba a rayuwar sa. Zaki yayi murna da samun wannan damar, domin kuwa akwai jikakiya tsakanin su.

Yayinda sukayi tozali da kurege, zaki yayi gurnani mai tsanani, amma kurege bai firgita ba, yace meme tsakain ka da 'ya'yan pakara?

Sai ya rika ja da baya kadan kadan yanayiwa zaki bayani. Yace watakila an gayama karya, abinda ya faru dai ina kare 'ya'yan pakara ne cikin rami na zo ma in nuna maka zurin. Sai suka juya cikin daji. Zaki yayi gunaki, sai kurege yayi tsalle ya fada cikin ramin sa domin tsirar da ran sa.

A daidai lokacin kuma an fara cida da tsawa, zaki bai son jika, sai ya tube kashin jikin sa, ya ajiye a bakin ramin kurege ya nemi wurin fake ruwa cikin daji. Yayinda aka fara ruwa sai gashin zaki na fadawa cikin ramin kurege, shi kuwa kurege yana zato har yanzu zaki ne ke tsaye bakin ramin sa. Amma daga bisani da ya dauki gashin sai ya iske ashe zaki bai bakin remin, sai ya fashe da dariya. Yace wannan gashin manyan dawa ne, ba abin tsoro bane, shine kurege yafito daga rami ya sheka a guje cikin daki.
*Shangani Folktale.*

**Yarinyar Da Mafarkin Ta Ya Zama Gaskiya: 3mins. 45secs**
(Wannan labarin hakika gaskiya ne ya faru, bayan hatsarin da ta samu lokacin tana yarinya amma ta cimma burin ta). A watan Mayun 1985, Sarah Doherty Kellet ta hau dutsen McKinley dake Alska ta kasar Amurka, amma ba wannan ne ainihim labarin ba na game da hawa kolouwar ddutse.

Lokacin da take yarinya Sarah tana sha'awar zama 'yar wasanin motsa jiki. Tayi ta samun horo sosai kan ninkaya dakuma tseren keke, haka kuma tana da sha'awar hawa dutse. Tana 'yar shekara 13 a 1973 ta sami hatsarin mota, wanda ta kusan mutuwa. Ba kamar yadda likitoci suka zata ba, Sarah ta rayu tayiu aiki tukuru inda ta sake samun lafiyar ta. Sarah ta fara shiga cikin gasar wasanin motsa jiki kadan kadan har ta fara samun kyautakan bajimta cikin gasar musakai. Haka kuma sha'awar ta na hawa dutse sai karuwa takeyi. Samun kan hankali ta fara da hawa kananan duwatsu, yayinda ta fara kwarewa game da hawa dutse. Yayinda ta fara kwarewa da sanin makaman hawa dutsen burin ta na karuwa. Sai ta fara rayawa a zuciyar ta game da hawa dutsen McKinley, wanda shine mafi tsawo a arewacin kasar Amurka, yana da tsawon mita dubu shida da 194 ga kuma tsananin sanyi can kololuwa.

Damar ta ta hawa dutsen McKinley tazo ne a shekarar 1985, lokacin da aka gayyace ta zuwa wajen gwajin kayan hawa duwatsu. An gayace ta ne saboda kudurin ta da karfin halin da take nunawa. Sarah anyi mata kayan hawa dutsen ne na musamman saboda nakasar ta, wanda take yi bisa kujerar guragu.

Ranar 29 ga watan Afrilu 1985 suka fara hawa dutsen. Ga Sarah ta fara ne lokacin da ta hau dutsen dake da daskararen kankare kimanin mita 4,900. Koda yake ga masu kafa ba abune mai tsayi ba, amma ga ita dake kan kejar guragu, tayi ta kokartawa dai. Sarah tayi ta hawa dutsen tare da sauran mutanen. Tawagar ta kafa sansani wajen nisan mita 5,243 kan dutse, sunko zauna nan har na kwananki uku, saboda guguwar da ta taso lokacin.

Ranar 19 ga watan Mayu, sararin samaniya ya wartsake, kana su ka cigaba da hawa. Sarah ta cigaba da yin duk abinda saura masu lafiya keyi. Bayan sa'o' 12 ne tawagar ta kai kiloluwa. Sarah burin ta ya cika tayi abin tarihi.

Kamar Sarah rayuwa tun mutum na karami ba koyaushe ke da dadi ba, amma duk da haka ba zai hana mutum more rayuwar sa ba muddin akwai kuduri. Muddin dai muka kuduri aniyar cika burin mu to kuwa zamuyi nasara komai rauni.
*AHI/Growing. Up.*